



Ali ba ya gani.

Amma kuma ba ya bara.

Ya ce bara ba kyau.




Ali ya je makaranta.

Domin karatu ya fi bara.


Bara na jawo raini.



Ali ya je makarantar makafi.

Sauran yara na mamakin Ali.


Makaho zai koyi karatu?



Ali bai damu da su ba.

Ya san zai iya karatu


kamar kowa.



Ali ya koyi karatu da


yatsa.

Ya koyi rubutu da na'ura.



Ali ya shiga jami'a.

Akwai makafi a jami'a.



Ali ya yi karatu.

Ya nace har ya zama lauya.



Makaho na karatu.

Makaho na rubutu.

Makaho na aikin lauya.